*KASHI NA DAYA*
*'YANCI DAGA*
*MASAR*

Darasi na 1

# JARIRI A CIKIN KWANDO

Fitowa 1:1-2:21; 2:1-10

**Alaman hannun Allah:**
**Allah Mai Iko ne, Mai Kauna kuma.**



**ME MUKE SO YARA SO KOYA A WANNAN DARASI?**

Za su:

* koya cewa Allah mai iko ne da kauna kuma
* sani cewa Allahn nan da ya lura da dan yaron nan Musa, yana kula da mu har yanzu.

**HADDACEWA**

"Sau daya Allah ya fada, san biyu na ji cewa Allah yake da iko. Madawamiyar kauna, ta Ubangiji ce"

Zabura 62:11-12

# SHIRIN MALAMI



***NAZARIN LITTAFI MAI TSARKI***

Mutanen Allah, zuriyar Yakubu, sun yi shekara 370 a Masar. Darajar da akan ba su saboda Yusufu, yanzu babu. Yanzu su bayi ne a kalkashin wani sabon Firauna wanda Karin yawan mutanen Yakubu yana tsorata shi. Lura da yadda Allah yana ji game da mutanensa.

- "…Na ga………….."
- "…Na ji……….."
- "…Na damu……."

(Fitowa 3:7-8)

Tuna fa, wannan zai zama mana ta'aziya a lokacin da muna cikin wahala.

Tuna fa, ba koyar da gaskiyar labari muke yi kadai wa yara ba. Muna so su ga ikon Allah da kaunarsa mara iyaka. ***Har zuwa yau, shi ne Allahn nan mai iko, mai kauna kuma!***



***ME MUKE BUKATA DOMIN DARASIN NAN?***

1. Hoto na 1. 'Diyar Fir'auna ta sami Musa' domin LABARI DAGA LITTAFI MAI TSARKI kashi na 3.
2. Domin GABATARWA, yi tunani a kan wata damuwar da ke fuskantar yara ko abin da ya dame ka. Ka shirya don ka ambace su idan yaran ba su fada ba. Suna iya jin kunyar fada a gaban sauran yara.
3. Domin GABATARWA, katuna biyu da rubutun IKO da KAUNA a kansu.
4. Domin LABARI DAGA LITTAFI MAI TSARKI kashi na 2, doli - dolin yaro ko ka gyara kamanin jariri da tsumma, kwandon da za a iya sa jariri a ciki.
5. Domin KARSHE, takarda da fensir ko launi domin kowane yaro.



# LOKACIN DARASI

**Gabatarwa** **A FARA DA ADDU'A**

- Yara su fadi lokacin da suna tsoro saboda abin da yake faruwa kewaye da su. Su tattauna abin da ya ke faruwa da yadda suka ji. Ba da misali da abin da ya faru da kai.
- YI musu tuni da kalmomin wakan nan: "Yesu ya iya, ya iya …" *Wadanne halayen Allah ne wannan waka ta tuna mana?* (wato, me wakar ta koya mana game da Allah? (Allah mai IKO ne). (**Malami**: nuna kati da aka rubuta wannan akai)
- NUNA — Kati da aka rubuta KAUNA akai tambayi yara su yi tunanin aya ko wakar da ta nuna mana kaunar Allah zuwa garemu.
- YI TAMBAYA — *Ta yaya tunawa da kaunar Allah da ikonsa zai taimake mu lokacin da muna tsoro saboda abubuwan da suke faruwa kewaye da mu?*

Labarin Littafi Mai Tsarki na yau yana kan wani iyali ne da suka yi rayuwa a zamani mai wuya. Bari mu dubi yadda suka ga kauna da ikon Allah wanda ya taimake su.

## 1. Mutanen Allah sun sha azaba (1:6-22)

- YI TAMABAYA - *wanene dan Yakubu wanda ya yi mulki a Masar wanda a karshe ya kawo iyalinsa?* (Yusufu ne )
- Iyalin Yusufu sun zo Masar saboda suna gudun yunwa. Sun dade da zama a wurin, sun yi yawa, su ne ake kira Israilawa.
- An yi wani sabon Sarkin Masar, ana kiransa Fir'auna. Shi da mutanensa suna tsoro kada Israilawa su mamaye kasar. Sun sa mutanen Allah a wahala. Suna yin tubula cikin zafin rana.
- Mutanen Allah suna da karfi kuma Allah ya taimake su. Iyalinsu sai kara yawa suke yi.
- KARANTA abin da Fir'auna ya fada wa Ungozoma na Israilawa da abin da suka yi - Fitowa 1:16-17.
- TATTAUNA yadda iyalan Israila suke ji idan an haifa masu 'ya'ya maza.

## 2. An boye Musa jariri (2:1-4)

- BAYYANA yadda wata mata tana da jariri mai kyau. Sun yi ta boye shi. TATTAUNA abin da uwar jaririn ta yi don boye shi — ta sa labule a taga, ba ta taba fitar da shi waje ba.
- RIKE doli– dolin jaririn da ka kawo yayin da kana ba da labarin. BAYYANA yadda jaririn ya fara yin karfi lokacin da yana girma. *Ta yaya wannan ya sa kulawa da shi ya zama da wuya?*
- KARANTA Fitowa 2:3-4. NUNA kwandon da ka kawo, ka BAYYANA yadda kwalta da aka sa a jikin kwandon zai hana ruwa samun Musa. Nade jaririn a cikin tsumma, ka sa shi a kwando.
- YI TAMBAYA— *A tunaninka, yaya 'yar'uwar Musa ta yi lokacin da aka sa Musa a kwando, aka sa shi bisa ruwa ita kuma ta tsaya tana ganinsa?* (Mai yi-wuwa ta ji tsoro amma ta yi karfin hali da ta tsaya don ta kula da shi.)

## 3. An sami kwando (2:5-6)

- Karanta Fitowa 2:5-6. *A ganinka, me Maryamu ta ke tunani lokacin da diyar Fir'auna ta sami kwan-don?* (Yara su fadi yadda ta yi. Ba da shawara cewa mai yiwuwa ta ji tsoro don tana ga idan an gane Musa dan Israila ne za a kashe shi).
- NUNA Hoto na 1.
- YI TAMABAYOYI da za su taimaki yara su yi tunani a kan yadda Allah yana aiki don sa sarauniya ta yi juyayin jaririn nan.

## 4. An kai Musa gun Uwarsa (2:7-10)

- KARANATA Fitowa 2:7. *Ko kana ji Maryamu ta same shi da sauki lokacin da ta ce za ta kira wata mata ta kula da jaririn?* (Allah ya ba ta hikimar sanin abin da za ta fada tare da karfin hali.)
- FADI yadda Maryamu ta kira uwarta da yadda sarauniya ta roke ta ta kula da jaririn. Maryamu da iyalinta sun ji dadin yadda Allah ya kare jaririnsu.
- RABA yara don su yi kwaikwayon Masarawa mugaye, Jariri Musa a ruwa, Sarauniya ta sami kwando, Maryamu ta kawo uwar Musa don ta kula da shi.

## Karshen Darasi ...

* TUNA wa yara yadda aka ambata a GABATARWA lokatan da muna iya jin tsoro. Allah ya yi alkawari zai tai-make mu lokacin da muna tsoro.

► **Koyar da Haddacewa yanzu (Zabura 62:11-12).** NUNA katunan nan biyu - IKO da KAUNA. *Ta yaya muka ga iko da kaunar Allah a hanyar da ya taimaki iyalin Musa? Ta yaya sanin cewa Allah mai IKO da KAUNA ne zai taimake mu lokacin da muke cikin hatsari?* (Idan mun tuna Allah mai iko ne, mai girma ne, kuma yana kaunarmu, zai ba mu karfin hali na fuskantar lokata masu wuya. Zai taimake mu yin shawara mai kyau kuma za mu yi abin da ya dace.)

* RABA wa yara takarda da fensir ko launi. Su zana ko su rubuta lokacin da sun ji tsoro sosai ko sun damu. Yara su rubuta kalmomin nan "Allah MAI IKO ne, mai KAUNA "kuma.

**ADDU'A:** Yara su yi addu'a da kansu. Su gode wa Allah saboda ikonsa da kaunarsa. Su roke shi ya taimake su lokacin da suna tsoro.

**WAKA:** "Allah Uban ne, ba zan ji tsoron kome ba"♫